OPEN ACCESS
Scholars International Journal of Linguistics and Literature
Abbreviated Key Title: Sch Int J Linguist Lit
ISSN 2616-8677 (Print) | ISSN 2617-3468 (Online)
Scholars Middle East Publishers, Dubai, United Arab Emirates
Journal homepage: https://saudijournals.com

Original Research Article

# Siddabaru Adon Damfara: Nazarin Damfara Jiya Da Yau

Suleiman Abdullahi Wamba[1]*, Hassan Salihu[1]

[1]Department of Arts Education, Hausa Section, Federal University of Education, Kontagora, Niger State

**DOI:** https://doi.org/10.36348/sijll.2026.v09i05.001 | **Received:** 19.02.2026 | **Accepted:** 13.04.2026 | **Published:** 02.05.2026

***Corresponding author:** Suleiman Abdullahi Wamba
Department of Arts Education, Hausa Section, Federal University of Education, Kontagora, Niger State

## Abstract

The study seeks to explore the olden days and contemporary tricks deployed by fraudlers in rubbing off their victims of their valuable possessions, money, food items etc. The study used both primary and secondary means in collecting its data and descriptive survey data analysis was used in order to analyses the study's data. The study revealed among other things that the fraudulent activities via tricking has negative effects on both the victims as well as their communities. The study also recommends that fraudlers be exposed among the communities and people should morally upright as there is no short-cut to richness.

**Keywords:** Siddabaru, Damfara, Jiya, Yau.

**Copyright © 2026 The Author(s):** This is an open-access article distributed under the terms of the Creative Commons Attribution **4.0 International License (CC BY-NC 4.0)** which permits unrestricted use, distribution, and reproduction in any medium for non-commercial use provided the original author and source are credited.

## 1.1 GABATARWA

Damfara daɗaɗɗen al'amari ne a cikin al'ummar Hausawa. Ana gudanar da wannan al'ada a matsayin sana'a a wasu mutane. Domin ba su da kowace hanya ta neman abinci da rufa wa kai asiri illa tunanin yadda za su yi damfara su karɓi kuɗaɗe a hannun mutane ko wasu ƙaddarori waɗanda za a iya sayarwa a samu kuɗi. Wannan damfara kullum sai sauya sabon salo take yi. Idan `yan damfara sun ɓullo da wata hanya, al''ummar Hausawa suka gane su, sai kuma su sake tunanin fito da wata sabuwa wadda al'umma ba su san da it aba, ko kuma sun sani amma sun manta.

Don haka, wannan bincike ya yi nazrin damfara a da da kuma yadda ake aiwatar da ita a wannan zamani. Karɓar kuɗi a hannun jama'a ta hanyar damfara abu ne mawuyaci, don haka sai an yi amfani da siddabaru wajen tafiyar da hankalin mutane kafin su amince su miƙa abin da yake hannunsu. Wannan siddabaru yana iya kasancewa ta hanyar kwaɗaiatar da su ko kuma ba su tsoro domin gudun yin hasara babba. `Yan damfara suna amfani da siddabaru da kuma taimakon `yan kore, wajen yin damfara. `Yan kore suna taka muhimmiyar rawa wajen yin damfara ta gargajiya da kuma ta zamani. Su ne suke nemo bayanai su kai wa `yan damfara sannan da suke a ke haɗa kai wajen nuna wa al'umma abubuwan damfara gaskiya ne. Don haka, suna jawo hankalin mutane wajen miƙa wuya a cikin sha'anin damfara har a samu sa'a su faɗa tarkon `yan damfara. Har wa yau, akwai `yan kore na gargajiya da na zamani, waɗanda suke taimakawa wajen yin damfara a cikin al'ummar Hausawa.

Duk da kasancewar yaɗuwar ilimin zamani da na addinin a cikin al'ummar Hausawa da kuma haramci da addinin Musulunci ya yi a kan cin dukiyar wani ba tare da haƙƙi ba, tare da kuma sanin illar damfara ga tattalin arziki da kuma rayuwar al'umma. Har yanzu al'adar damfara tana ci gaba da wanzuwa a cikin al'umma. Dalilai da dama suna haifar da faruwan damfara daga ciki akwai son kuɗi cikin gaggawa, wanda shi ne babban tarkon da `yan damfara suke amfani da shi. Daga wannan sai kwaɗayi, wanda Hausawa suke cewa mabuɗin wahala. Waɗannan suna daga cikin dalilan da suka yi sanadiyar damfara a cikin al'ummar Hausawa. Bayan haka, akwai illar da damfara take yi, ga wanda aka damfara da kuma tattalin arzikin ƙasa baki ɗaya.

### 1.2 Manufar Bincike

Babban manufar wannan bincike ita ce, yin hannunka mai sanda ga al'ummar Hausawa game lamarin damfara a da, da kuma yadda ake gudanar da shi a yau. Saboda haka manufar ta kasance kamar haka:

i. Fito da yadda ake yin damfara na gargajiya da na zamani.
ii. Faɗakar da al'ummar Hausawa a kan sabbin hanyoyin damfara na zamani da yadda za su kauce masu.
iii. Fito da dabarun da `yan damfara suke amfani da su wajen cim ma burinsu na karɓar kuɗaɗe a hannun mutane.
iv. Fito da illar damfara ga ɗaiɗaikun mutane da kuma tattalin arzikin ƙasa.
v. Bayyana dalilan da suke haifar da damfara a cikin al'umma.

### 1.3 Dabarun Gudanar da Bincike

A wajen gudanar da wannan bincike an bi hanyoyi daban-daban wajen tattaro bayanai. Daga an yi amfani da manya da ƙananan hanyoyi. Hanyoyin su ne:

i. Hanya ta farko da aka fara bi wajen gudanar da wannan bincike ita ce, nazartar littattafai da aka wallafa waɗanda suka danganci dabarun damfara jiya da yau. Waɗannan littattafai ba lallai ne su yi magana kan dabarun damfara kai tsaye ba, salon da suka yi amfani da shi a wurin fito da waɗannan hanyoyi da za a iya cin karo da su, za su taimaka wa binciken.
ii. Binciken ya yi amfani da kundaye na digiri na farko da na biyu da kuma na uku, domin tsamani cin karo da waɗanda suka tsakuro wani abu daga cikin irin dabarun da `yan danfara suke amfani da su don wajen damfara na gargajiya da na zamani.
iii. Haka kuma, binciken ya waiwayi mujallu daban-daban har da waɗanda aka saka a yanar gizo. Hakan ya taimaka wa wannan bincike don cim ma nasara.
iv. Binciken ba zai yi tuya ya manta da albasa ba, ya zama wajibi a tuntuɓi masu ruwa da tsaki masana waɗanda suka jiya suka ga yau a kan irin waɗannan hanyoyi na damfara na gargajiya da na zamani da kuma waɗanda suka faɗa tarkon mayaudara musamman na zamani.

### 1.4 Bitar Ayyukan da suka Gabata

Masana da manazarta da dama sun tofa albarkacin bakinsu game da abin da ya shafi damfara ta gargajiya da kuma ta zamani. Daga cikinsu akwai Bunza (1986) da Bunza (1994) da Maiyama (2008) da Sani & Yusuf (2024) duk sun tattauna yadda damfarar Bahaushe take ta gargajiya da kuma ta zamani. Binciken na su ya kasance tamkar fitila ce mai haskawa ga wannan bincike. Don haka, wannan aikin bincike ya amfana ƙwarai da waɗannan ayyuka na masana.

### 1.5 Ra’in Bincike

Ra’i falsafa ce da ake amfani da ita wajen yanke hukunci a kan gaskiyar yadda abu yake faruwa (Ado, 2019:30). Don haka da ra’i za a yi amfani a yanke hukunci a kan manufar wannan bincike. Bisa wannan dalili, aka ɗora binciken a kan ra’in fanɗarewa daga karɓabbun al’adun al’umma (Deɓiance Theory). Fanɗarewa daga al’adun al’umma shi ne aikata wata ɗabi’a wadda ba ta yi daidai da ɗabi’un da al’umma ta keɓance a matsayin karɓaɓɓun halaye ba (Radda, 2014:151). Wani Bature mai suna, Geofry Leach (1969) ya fara amfani da wannan ra’i a wajen nazarinn harshe da adabi. A ɓangaren nazarin al’ada kuwa, wani Bature mai suna Emile Durkhain shi ne ya fara yin amfani da ra’in. Daga nan kuma, sai aka samu magajin Emile Durkheim, Robert K. Merton (1957) ya ƙara faɗaɗa nazarin fanɗarewa daga al’adun al’adun al’umma, (Ado, 2019:119).

Wannan ra’i ya yi daidai da wannan bincike domin binciken yana bayani ne a kan yadda wasu al’umma suka fanɗare wa kyawawan al’adun Hausawa, saboda su mallaki kuɗi ta hanyar damfara. Sannan duk abubuwan da suke aikatawa ya saɓa wa ɗabi’u da halayen Hausawa da aka sani tun shekaru aru-aru da suka gabata.

### 2.1 Ma’anar Siddabaru

A hasashen Bunza, (1989:67) Siddabaru ba hastin bara ba ce, watao kalma ce ta Hausa tsintsa don haka ne ma masanin ya bayyana ta da waɗannan abubuwa:

i. Cukurkuɗa abubuwa ko kuma rikita su tare da ɓatar da bakin zare. Idan mutum ya cika sassarƙe bayani, ana cewa ya cika siddabaru a zancensa.
ii. Wayo da dabara wajen kare kai, ko kuɓutar da kai daga wani abu. Da za a koro ɓarawo ya shiga nan ya fita can, har ya dubultar da masu nemansa, a ce, ya yi masu siddabaru.
iii. Hikima da basira ta fuskar ƙagen wasu abubuwa. Domin kuwa yau saboda ci gaban wannan ƙarni, da an ga jirgin sama ko rediyo ko salula (wayar hannu) ko mota a kan ce siddabarun Bature ne.

A ra’ayin Adamu, (2014:38-39) siddabaru shi ne, sanin yadda za a yi wasa da hankalin mutum har ya yi mamakin yadda abubuwa ko ayyuka suka faru.

A taƙaice dai ssiddabaru yana nufin zunzurutun wayo da ɓatar da hankalin mutane a kan wani abu ko a shagaltar da mutane a aiwatar da wani abu wanda bai san yadda aka yi shi ba.

#### 2.1.1 Ma’anar Damfara

Damfara kalma ce Bahaushiya ba hatsin bara ce, ma’ana kalma ce ta Hausa ba aron ta aka yi daga wani harshe ba. Masana da manazarta al’ada sun tofa albarkacin bakin su a kan ma’anar damfara, daga cikin akwai: Maiyama, (2001:27) ya bayyana damfara da cewa:

“Hanya ce da wani ƙwararre yake bi ya mallaki abin mutum ta hanyar amfani da daɗi lafazi da nuna kwaɗayi zuwa ga wanda za a zalunta don ya yarda ya saki jiki har ya amince don ƙwaɗayin abin da aka yi masa nuni da shi”.

Shi kuwa Bunza, (1994:2) cewa ya yi:

> *“*Amfani da dabara ta fuskar nuna wayo da yaudara a kaikaice domin a karɓi dukiyar mutum. Damfara ta keɓanta ga kuɗi tsabarsu ko wasu ƙaddarorin da ake iya kaɗarwa nan take a sami tsabar kuɗi. Da yawa takan samo asali ne daga kawo kuɗi in yi maka kuɗi ko alƙawarin samun kuɗin cikin sauƙaƙƙar hanya”.

Shi kuwa Ƙamusun Hausa (2006:92) ya bayyana damfara da yaudara ko zamba da ake yi wa wani mutum da yake zaton zai sami wata ƙaruwa. A yayin da Adamu, (2014:118-119) ya kalli damfara a matsayin wata hanya da mutum zai shirya ta wayo da ƙarya domin ya karɓi abin hannun jama'a.

A fahimtar wannan bincike, damfara hanya ce ta karɓar kuɗi a hannun mutane ta amfani da siddabaru da ƙwaɗaitar da mutum bisa samun abin duniya cikin sauƙi. Waɗannan hanyoyi sun haɗa da dabarun gargajiya da na zamani.

### 2.1.2 Dangatakar Siddabaru Da Damfara

Dangantakar da take tsakanin siddabaru da damfara ta jini da tsoka ce. Domin kuwa damfara ba ta gudana sai an haɗa da siddabaru, don ta hanyar siddabaru ne ake jawo hankali mutane har a damfare su. Wannan ya yi daidai da bayanin da Bunza, (1989:89) ya kawo a kan yadda ake amfani da siddabaru wajen yin damfara. Misali siddabarun rubutu cikin ruwa, wanda malaman tsibbu suke yi wajen damfarar masu neman maganin zana da baduhu. Yadda suke yi shi ne za su sami wata farar takarda a saka a cikin wani kasko da wani kasko kamar sa sai a rubuta wasu ayoyi a kaskon da aka rufe da farar takarda a ciki, a cikin ruwa. Idan an buɗe sai ka ga takardar da take cikin ruwa da rubutun da aka yi a kan kasko ya fito a cikinta, cikin ruwa ɓaro-ɓaro, kuma har a ɗauko takardar a karanta.

Wannan siddabarun shi zai taimaka a yi damfara domin in ba a gwada wa mutum abin da hankalinsa ya kasa ganewa ba, ba zai aminta ya ba da kuɗi ba. Saboda haka, duk inda za a yi damfara to sai an fara yin siddabaru don ita ce adon damfara. Wannan ya tabbatar da maganar Adamu, (2014:47) inda yake cewa hanyoyi nuna wayo da dabaru waɗanda sukan kauce hankulan mutane su ne suke ɗaukar siffa ta siddabaru a sha'ani na damfara a ƙasar Hausa.

### 2.1.3 `Yan Damfara

`Yan damfara kamar yadda Bunza, (1989:269) ya bayyana cewa su ne mutane masu yawo wuri-wuri ba su sayar da wani magani illa yawon damfara a birane da ƙauyuka. Sukan yi wa mutum kuɗin jabu ko su yi dabon kuɗi nan take, ko su ce za su yi wa mutum dukiya. Wasu sukan shirya mota ta kara su sihirce ta su sayar wa mutum, sai ya shiga sai ya ga kara.

To, a duk lokaci da za a yi damfara tilas ne sai an samu `yan kore domin su ne kanwa uwar gami. To wane ne ɗan kore? Mene ne matsayinsa a wajen gudanar da damfara.

### 2.1.3 Ɗan Kore A Wajen Damfara

Ɗan kore shi ne kanwa uwar gami a wajen aiwatar da damfara. Domin duk wani abu da ya gudana ɗan kore ya shirya shi ya kuma aiwatar ta yadda hankalin mutane ba zai gano abin da ake nufi ba. Don haka Bunza, (1989:23) ya bayyana ɗan kore da cewa shi ne mai koro wa ɗan damfara mutane ana karɓar dukiyarsu. A hasashensa an samo wannan suna ne daga mai kiro jama'a. Wato ɗan kore yakan kasance namiji ko mace, babba ko yaro, ɗan gida ko baƙo wanda zai dinga taimaka wa ɗan damfara a kaikaice ba da sanin mutane ba. Kusan duk abin da yake bayan fage da sanin ɗan kore kuma duk wata damfara da za a yi a bayan fage ko abu ya faɗo daga sama ko a ji ƙarar shi da dai sauran su duk da hannun ɗan kore. Ɗan kore dole ya zama mai wayo, mai natsuwa da gaggawa ga aikata duk wani aikinsa ba da ɓata lokaci ba. Kuma an fi son ɗan kore ya zama ba sananne ba ne a idon mutanen gari. Idan so samu ne a wani lokaci an fi son baƙo, a wani lokaci ko ɗan gari sai a ƙulla da shi indai ba sananne ba ne a idon jama'a. Ɗan kore yakan yi shiga daban-daban, wani lokaci yakan yi shigar ƙauyawa, yakan kuma saka kayan Fulani, a wani lokaci yakan yi shigar yara gayu ko ya yi shiga ta siffar malamai da dai sauransu. Idan ɗan kore ya ƙware sosai babu yadda za a yi jama'a su gane cewa haɗin baki aka yi da shi a cuce su. Idan ɗan kore ya iya taka rawarsa sosai ɗan damfara zai tara kuɗi mai yawa. Bunza, (1989).

### 2.1.4 Matsayin Ɗan Kore A Damfara

Ɗan kore yana da muhimmancin ƙwarai da gaske wajen gudanar da damfara. Shi ne yake fara nuna wa mutane cewa abin da aka nuna masu gaskiya musamman ta hanyar siddabarun dandali. Idan ɗan damfara ya nuna wa mutane kuɗi a bayyane yana cewa, "Ina mai naira ɗari ko ɗari biyar", alhali a hannunsa akwai naira dubu ko dubu biyar. Cikin ɗan lokaci idan naira ɗari ce sai ka ga wani ya zo ya ce, 'na saya naira dubu'. Bayan ya riƙe hannusa sai ya ce, "Malam ban sayar ba". Bayan ya saki hannunsa sai ka ga naira dubu ta koma dubu biyar nan take.

### 2.2 Dalilin Yin Damfara

Hausawa sukan ce, "Banza ba ta kai zomo kasuwa". Haka kuma, ruwa ba sa tsami banza. Dangane da wannan akwai dalilai da dama da suka haifar da wanzuwar damfara a ƙasar Hausa. Dalilan kuwa su ne:

a. Kwaɗayi: Hausawa sukan yi karin magana suna cewa, 'kwaɗayi mabuɗin wahala'. Wannan haka yake domin dogon guri ga rayuwa kan haifar da rashin dangana da wadatar zuci wanda kan yi sanadiyar faɗawa tarkon damfara. Tsammanin son wani abu wanda mutum bai mallaka ba ko son karɓar abu cikin a wajen wani mutum shi yake jefa mutane cikin damfara tsundum (Adamu, 2008, & Maiyama, 2001). Wannan bayani ya yi daidai da abin mawaƙi Muhammadu Ɗanƙurji yake cewa:

:Lantana jikanyar Buhari Aljannan makaɗa.
…………………………………………….
:Ɗan Malam Bawa mai mahaukaciyar biɗa,
:Ga ka da fam goma ka ga ƙwanjan sule guda,
:Har ka tsaya mai sule guda yana maka sababi

(Muhammadu Ɗanƙurji: Waƙar `yan caca).

b. Son banza: Duk ɗan damfara yana son banza, haka shi ma wanda aka damfara son banza ya

kai shi. Domin hangen abin da yake hannun wani da raina nashi, shi ya kai har ka damfare shi.

c. Neman arziki dare ɗaya: Sau da yawa mutane sukan tsunduma cikin harkokin damfara saboda neman arziki cikin sauƙi babu wahala. Haka wanda aka damfara, tun da sun ga kuɗi ruwa-ruwa ana facaka, su ma sukan shiga ko sa samu nasu (Adamu, 2008).

d. Nuna bajinta: Nuna ta maza ko kuma aikata wani abin da duk ba kowa zai iya ba yin sa ba da son ayaba shi ke haddasa mutum ya shiga harkar damfara ta hanyar amfani da siddabaru da kuma amfani da na'urar zamani.

e. Bushewar Zuciya: Wannan shi ne Yahya, (1994 da 1996) ya kira da rashin imani wato rashin tausayi. Rashin imani yake haifar da bushewar zuciya. Idan zuciyar mutum ta bushe, wannan na iya sa mutum ya aikata duk wani abin assha da tir. Bayan kasancewar ɗan damfara mai cutarwa da rashin sanin ya kamata mutane suna masa kallon maras tausayi da guma baƙin ciki.

f. Rashin Aikin Yi Ga Mutane: Rashin abin yi ga mutane yakan haifar da zaman kashe wando. Zaman kashe wando zama ne na jiran tsammani na jiran Allah ya ba ku mu samu. Akwai tabbacin cewa irin wannan zama na iya kai wa ga lalaci da yin damfara. Domin duk lokacin da zaman banza ya yawaita, mutuwar zuci kuwa za ta rufa baya a ƙarshe abin da zai faru shi ne rashin ɗiyauci. Matuƙa mutum bai da aikin yi, bai kuma ƙirƙiro wa kansa ba aikin da zai amfane shi ba to shi ƙarshensa damfara. Wannan ya zama tilas domin babu rayuwar da za ta iya tabbata cikin talauci da rashi, gashi kuwa tana ganin jama'a na kai kawo da harkokin kuɗi ba ta san ranta (Maiyama, 2001).

### 3.1 Damfarar Gargajiya

A gargajiyance, akwai hanyoyi da ake bi wajen damfarar mutane kuɗaɗensu ko kuma wasu ƙaddarorin kuɗi. Wannan ita ce nau'in damfara wadda Hausawa suke gudanar da ita ta hanyar amfani da dabarun gargajiya. Kuma wannan damfara tana gudana ne a wuraren daban-daban, sannan kuma sukan yi ƙaryar ba da magani, kamar yadda Bunza, (1989:45) ya ce, "Ba sayar da wani magani suke yi ba illa yawon damfara, a birane da ƙauyuka". Wannan nau'i na damfara ta kasu kashi-kashi kamar haka:

#### 3.1.1 `Yan Wala-Wala

`Yan wala-wala mutane ne da suke amfani da wuri ko da takarda ko kati mai launin alamu, su juya su ta hanyar dabara don su yaudari idon mai kallo da taimakon `yan kore. Wala-wala caca ce wadda ake sa mai kwaɗayi ya zaɓi kati, in ya yi kuskure dole ya biya kuɗi (Alhassan da wasu, 1982:88).

`Yan wala-wala su ne `yan damfara da suka fara fitowa a ƙasar Hausa bayan bayanar Turawa a wannan ƙasa [1]. Wala-wala da kati ake yin ta, irin katin da ake caca da ita. Sukan shiga kasuwa su a je dandalinsu musamman a wuraren da ake yin ciniki sosai na awaki ko shanu ko dai wani abu mai kama da haka. Sukan nuna wa mutum kati a fili suna cewa:

"Wannan mai ci, wannan babu,
Idan ka ɗauki wannan ka ɗauki mai ci,
Idan ka ɗauki wannan ka ɗauki banza".

Akan samu `yan kore masu ƙoƙarin nuna wa wanda bai sani ba, mai ci. `Yan koren nan sun san duk katin sosai da sosai. Da yawa sun sha haukata ƙauyawa suke zuwa da dukiya mai yawa kasuwa. Ana ce da su `yan wala-wala saboda yawan yawon da suke da hannuwansu wajen yin amfani da katin da lalewa da bazawa a ƙasa. Sukan ce, "Wala-wala ya ci ka" idan sun ci mutum, shi ya sa ake kiransu `yan wala-wala. (Maiyama, 2011:28)

A wasu lokuta `yan wala-wala sukan aro kuɗi hannun mutum sai su yi a ci, don ka gani wai kasa da kanka. Sun riga sun kiyaye duk katin, ko ka ga sun a je shi a gabanka ko ka ɗauka sai ka tarar ba mai ci ba ne.

#### 3.1.2 `Yan Kalambe

Kalambe kwali ne ake yi wa zane-zane da hoton abubuwa da dama kamar kada da tsari da damo da mota da keke da shamuwa da maciji da sauransu. Za a huje tsakiyaarsa a saka icce da waya a yi mata ƙugiya a jiye a yi rami a yi mata turke. Mai buga kalamben zai zauna a kan turmi ƙafafunsa na ƙasa, yana mazaya abubuwan kalamben na gewaye kamar tayar keke da gudu. (Maiyama, 2011:28 a cikin Bunza, 1989).

Ɗan damfara kan fara sa kuɗinsa `yan korensa su sa nasu, sai ƙauyawa da masu son kuɗin banza su yi tasa nasu. Duk hoton da ƙugiyar ta nuna mai hoton ne ya ci. A irin wannan damfarar mai buga kalamben da ke zaune da ya ga hoton da ɗan kore ya zaɓa sai ya ɗaga guiwarsa ya tsayar da wayar a hankali ba da sauri ba, yadda ɗan kallo ba zai fahimta ba. Yanzu irin wannan damfarar a ƙauyuka ne kawai ta ke ci ko a cikin yaran da ba su san ciwon kansu ba. (Doma, 2018:23).

#### 3.1.3 `Yan Marmashe

`Yar marmashe dai ita ce damfarar da ake yi a fili ƙuru-ƙuru a idon jama'a. Mai damfarar zai ɗauko yagaggun takardu ne ya ce, ina mai saya naira goma, ga kuma naira ɗari a cikin hannusa ana gani. A wasu lokuta kudin na ƙaruwa kamar dai a ce magani ne alhali dabaru ne kawai. Bisa gaskiya idan mutum ba ɗan korensu ba ne

---

[1] Bunza, (1994) "Damfara Da 419 A Bahaushiyar Al'ada" (Nazarin Nasonsu da Damabalarsu A Rubutattun Qagaggun Labaran Hausa). Takarada da aka gabatar a taron qara wa juna sani a jami'ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato.

ba zai ci nasara samu kamar sa. Yadda suke wannan damfara shi ne idan mai damfar ya ce wa zai saya? Sai wani ɗan kore zai zo ya ce, "na saya biyar". Bayan ya riƙe hannunsa sai ya ce: Malam ban sayar ba. Bayan ya sake hannunsa sai ka ga kuɗin ya koma naira arba'in ko naira ɗari nan take. A koyaushe a irin wannan damfara mai suna, 'Marmashe' duk wanda ka ga ya faye ci to, ɗan kore ne. idan kuma mutum ba ɗan kore ba ne, ko ka ga ya ci ana so a jawo hankalinsa ne a yaye shi sosai. Shiga-shigo ba zurfi ne kawai. Kuma duk wanda ka ga ya riƙa hannunsa sai yawan kuɗin ya ƙaru shi ma ɗan kore ne, shi ya miƙa kuɗin a lokacin da suka haɗa jiki cikin ɗan lokaci ƙanƙane kuma ana yin aikin cikin hanzari da wayo sosai (Bunza, 1994).

**3.1.4 Damfarar Dabo**

Masu wannan damfara sukan yi kuɗi ne, ko su tono su daga cikin ƙasa, ko su karɓo su daga sama. Suna kuma iya cika wani abu da su, a gani kamar da gaske. Wato sukan yanka fararen takardu su zama kuɗi. Amma a zahiri ba haka yake ba kau da ido ne, domin yawancin lokuta da sun ba mutum kuɗi za su ɓace ko kuma su koma takarda ko ganye. Suna nuna wa mutane gawar jikinsu a cikin ruwan masaki ko kwartanniya, sannan su shawarce su a kan yadda za su yi su kuɓuta daga halaka. A kan kira masa maƙiyinsa a nuna masa a gabansa. Wasu kuma sukan saka ƙwai a cikin kwalba ya kuma yi magana. Bayan haka ana harhaɗa wasu abubuwa a tada wuta ko a fitar da ruwa, ko a fitar da wani wuri ko wani abu, kamar a fitar da zinari ko azurfa daga wani wuri ko daga jikin kowane abu, ko a yi ruwan kuɗi ko a nuna dabbobi ko wani abin hawa kamar jirgin ruwa da mota.

Haka nan kuma suna iya juyar da murya wadda ba a sanin mai ita, ko su nuna wa mutum abubuwan fake, kamar kiran sarkin Aljannu, a yi magana da shi baki da baki, ko mayar da ƙarhu ko jela ko wata igiya ta zama maciji, ko a mayar da sansami ko ganye ko wani abu kuɗi wanda ake amfani da su a wannan lokaci. Ana iya canza kamannin mutum, kamar gajere ya zama dogo, ko ramamme ya zama mai ƙiba ko marar lafiya ya ji ya warke, da sauran siddabaru da suke yi don su damfare mutane da su.

Duk wannan damfara ba yiwuwa sai da siddabaru saboda abubuwan da suke yi tsagwaron wayo ne kawai ba tsafi ba ne. `Yan siddabaru sukan yi amfani da ƙahon rago ƙarami su sami takalman soso, su soka allurai kamar ɗari a soson, sai su saka shi a cikin ƙaho. Bayan wannan, sai su rufe ƙahon da wani marfi daban, a yi wa marfin huda gwargwadon yawan allurai da ke cikin ƙahon. Kuma za a yi saiti daidai yadda da an ɗauko ƙahon, aka jirkita kaɗan, sai a ga allurai sun turo kansu da yawa amma ba za su fito ba, domin suna ɗaure a can cikin ƙahon.

Bayan an shirya wannan ƙaho sai mai siddabaru ya shiga damfara yana karɓar kuɗin mutane. Idan ya tara kuɗin mutane da sunan ba su wani abu, sai ya ce ya fasa, can sai wani mutum ya fito ya ce, "Wallahi bai amince ba, sai an biya shi kuɗinsa, nan take sai ɗan siddabaru ya ce, "Zan harbe ka da allura". Ya zaro ƙaho ya fito da alluran, ya yi ihu sai a ga mutumin ya faɗi yana kuka, ga allurai a rigarsa da hularsa da wandonsa a sassaƙe, ga su ko'ina a suturarsa daɓa-daɓa. Hausawa sun ce, gani ga wane ya isa wane tsoron Allah. Da zarar mutane sun ga wannan sai su riƙa cewa, "Mun yafe" a dinga suɗaɗewa ana tserewa da ɗaiɗai da ɗaiɗai. Amma a zahirin gaskiya mutumin da ya zo ya ce bai yarda ba ɗan kore ne. kuma dama kafin ya shigo fage ya sossoka allurai a suturarsa a ko'ina yadda idan mutum ya gani sai abin ya ba shi tsoro da mamaki ya kuma zaci cewa lallai mai magani ne ya harbe shi da allurai. Yana fito wa sai ɗan siddabarun ya yi hito ya ciro wani ƙahi da allurai suke ciki ya ce ya harbe shi, shi ko ɗan koren ya faɗi (Bunza, 1989).

**3.1.5 Damfarar Zamba Cikin Aminci**

Alhasan, da wasu (1982:47) sun bayyyana wannan damfara da cewa, ita ce ake yi wa mutum idan mutum ya kawo kuɗinsa ajiya, domin zai haɗu da wani mutum mai albarka. Akan yi wa mutum dabara a nuna masa sani da sabo, inda a kan kira sunansa da na iyayensa, da garinsu, da sana'arsa da kuma buƙatar da ya sa wa gaba a ransa. Akan kuma yi wa namiji ƙifƙiftau da mace, a dibirce shi, ko a yi da mace ko da wani mai kuɗi ko sarauta ko ilimi, ta hanyar zamba cikin aminci. Wannan duk yana faruwa ne ta hanyar ɗan kore wanda zai ba da bayanin mutumin da buƙatarsa tun kafin ya zo wurin. Sannan kuma shi ne zai turo wannan mutumin zuwa wannan wurin domin biyan buƙatarsa. Misali wannan damfara shi ne kamar yadda Maiyama, (2008) ya kawo misali a cikin Littafin *Ruwan Bagaja* inda Alhaji Imam ya yi Malam Zulƙe wayo ya damfare shi a lokacin da suke cikin tafiya tare, sai ya kwashe labarin yadda ya samu kuɗinsa kaf ya shaida wa Alhaji Imam saboda aminci. A lokacin da Malam Zulƙe zai tsaya ratsi sai ya ba Alhaji Imam kuɗi ya riƙe mashi, amma da ya dawo ya buƙaci kuɗinsa sai Alhaji ya hana shi, ya ce, 'kuɗinsa ne'. Haka kuma wani misali na fito da damfarar zambo-cikin-aminci a lokacin da ɓarawo ya zo yi wa Alhaji Imam sata sai Alhaji ya yi amfani da wannan dabara ta zambo ciki aminci, ga yadda abin ya kasance:

> "Maraba, maraba. Ga tabarma ka zauna. Ashe za ka zo ka ƙi gaya mini tun da rana da muka gamu a kasuwa. Alhaji ya ci gaba da cewa, "Na yi ta yi masa magana kamar na san shi.
>
> Da ɓarawo ya fahimci nuna sani ya yi yawa, sai ya ce, "Ina ka san ni?'.
>
> Shi kuma Alhaji ya ce, 'ai tuni na san ka, bari ta kai ma duk danginka na san su, duk kuwa sun san ni'.
>
> Da ɓarawo ya ga da gaske Alhaji yake yi sai ya ce wa Alhaji, "Kai in ka san ina sunana?'. Sai Alhaji ya ce, "Na yi ihu da ƙwarai na ce, 'ai sunanka, 'Ɓarawo".

Muna iya cewa Alhaji ya yaudari wannan ɓarawo ta hanyar nuna sani wataƙila ba don ya yi amfani da wannan hanyar damfara ba da ɓarawo ya cuta masa.

Don haka ana ganin Alhaji ya yi amfani da wannan hanya ce don ya kori ɓarawo.

To, haka masu yin wannan damfara ke yin amfani da nuna sani a fili domin su damfari mutum. Don haka a lura duk lokacin aka ga mutum yana ƙoƙarin nuna wa wani sani ƙarfi da yaji ya dace a tuhumi wannan mutum sannan kuma kada a yi saurin amincewa da shi domin gudun faɗawa tarkon damfar zambo cikin aminci.

**3.1.6 Damfarar Gada-Gada**

Wannan nau'in damfara kamar yadda Maiyama, (2008:68) ya riwaito Bunza, (1994) cewa ita ce damfarar da ake yawo da hankalin mutum da dibirta shi wanda akasari aka fi yi wa baƙi waɗanda ba su san gari ba. Kuma masu yin wannan damfarar wasu lokuta sukan shiga rigar hukuma. Misali idan mutum baƙo ya zo yana neman wani wuri musamman mutumin karkara wasu `yan birni kan yi amfani da wannan damar wajen damfarsa. Misalin wannan shi ne lokaci da Malam Haruna da Maikuɗi suka tafi birni duba ɗan uwansu da hukuma ta kama. Ga yadda abin ya kasance:

> "Malam Haruna da Maikuɗi suka yarda saurayin ya wuce gaba suka bi shi. Ya shiga wannan lungu da su ya fita wancan har dai suka gaji da tafiya. Har Malam Haruna ya ce, "Shin samari har yanzu ba mu zo wurin ba ne?"

Ga abin da ɗan banzan ya ce:

> "Kada ka gaji baba, ai wurin ne da `yar tazara, amma mun kusa zuwa. To, ba don kun same ni na ɗauki ɗawainiyar kawo ku ba, da ya za ku zo nan da kanku". Bayan `yan tafiya kaɗan suka iso wani ɗan fili sai gogan ya ce, to, sai ku tsaya nan in je in sanar da masu gadin ga ku kun zo, in yi muku iso.

Jin kaɗan saurayi ya dawo ya koma ya ce, to, na shaida masu. Amma da ƙyar da lalama daban baki suka yarda. Kun yi sa'a da cewa suka yi wai tikitin rasil ɗin shiga ya ƙare sai jibi. To, amma tunda sun yarda sai ku kawo kuɗin tikitin rasil na Naira huɗu ku biyu ke nan.

Malam Haruna ya sa hannu ya ɗauko jakarsa ya kwance ƙullin ya zazzaro Naira huɗu ya miƙa masa. Bayan ya ga ya damfari ƙauyawa sai saurayin ya koma bakin ƙofar kurku ya ɗan jima kaɗan sai ya dawo ya miƙa wa Malam Haruna da Maikuɗi waɗansu `yan guntayen jajayen takardu guda biyu ya ce, 'To ga tikitinku na rasil. Ku je ku shiga kawai. Sai Malam Haruna suka karɓi wannan rasil suka kuma gode nasa. Ba su san cewa ɗan saurayi damfararsu ya yi ba.

**3.1.7 Damfarar Gardawa**

Gardawa suna nuna siddabaru da waibuwa iri-iri domin su damfari mutane. Suna gwada abubuwa kamar cin kasuwar sama, ko ƙone yaro da yanke shi, a warkar da shi, ko a ƙona tufa daga baya a fito da ita. Kuma ana iya shiga cikin wata dabba a fita wani wuri ko su shuka duma ko kabewa ya tsiro ya yi yaɗo da `ya`ya nan da nan. Ana iya kuma saka wuƙa cikin baki a fitar da ita ta hanci ko a karɓo wani abu daga sama Bunza, (1986).

**4.1 Damfarar Zamani**

"Zamani abokin tafiya, idan zamani ta ɗinka riga tilas ne a sa". Damfara ta shiga cikin tafiyar zamani, domin lokacin da ake ganin an samu ilimi da wayewa ta ƙara yawa, a lokacin ne mutane suke ƙara fito da sabbin hanyoyin damfara. Sannan samuwar na'urori da ci gaba zamani su ne suka haifar da damfara zamani. Damfara ta shiga hanyoyin zamani kuma babu wanda yake tsallake wannan nau'i na damfara. Ma'ana da jahilai da masu kuɗi da masu ulimi duk suna faɗawa cikin wannan tarko.

**4.2 Hanyoyin Damfara Na Zamani**

Akwai hanyoyi da dama da ake amfani da su wajen gudanar da damfara ta zamani waɗannan hanyoyi su ne:

**4.2.1 Ta Hanyar Satar Bayanan Sirri Na Asusun Ajiyar Kuɗi A Banki**

Mutane da dama sun samu kansu cikin rigima da bankunansu ta hanyar bayar da bayyanin siiri a kan asusun ajiyar kuɗinsu na banki. Dabarar da `yan damfara ke amfani da ita, ita ce ta hanyar kiran mutum a waya, su ce daga banki ne, ana buƙatar ya ba da lambar sirri wato PIN [2], ko lambobi huɗu na ƙarshe a katin ATM. Da zarar sun sami abin da suke buƙata sai su washe asusun nan take.

A wasu lokuta sukan tura saƙo a wayar mutum cewa daga bankin da yake hulɗa da su ne, akwai matsala a asusun ajiyarsa don haka ya kira wannan lambar domin warware wannan matsalar. Idan mutum ya kira su za su buƙaci muhimman abubuwa da suka shafi asusun ajiyarsu, idan aka yi rashin sa'a suka samu nan take sukan kwashe kuɗin ajiya daga asusun. Haka kuma akasari sun fi yin wannan damfarar ranar da banki ba su aiki. Don haka kafin ranar da za a kai ƙorafi a banki sun riga sun kammala nasu aikin na damfara.

Akwai wasu mutane da kan zo su tsaya a injin na cire kuɗi wato ATM [3], suna ƙoƙarin satar lamar sirri na mai hulɗa da banki. Idan kuma sun yi sa'a wanda ya zo cire kuɗi bai iya amfani da na'urar ba kuma ya nemi taimakonsu, sannan ya nuna masu lambar sirrinsa. Daga nan shi ke nan sun dinga ɗiban kuɗinsa sai in ya je banki

[2] Lamba ta sirri da kowane bai ajiya a banki yake amfani da ita wajen cire kuxi.

[3] Na'ura da ake liqa wa a bango a bakin baki wanda mutane ke zuwa suna cire kuxi. Da Turanci a cewa, Automated Teller Machine.

ya kai ƙorafi an toshe wannan asusu. Mutane da dama sun faɗa cikin wannan tarkon [4].

#### 4.2.2 Damfara Ta Hanyar Mutuwa da Neman Taimako

Wannan ita ma wata hanya ce ta damfara, a kan turo saƙon Imel ko kuma a kira mutum kai tsaye daga wata ƙasa ana shaida maka cewa wani bawan Allah ya mutu kuma ba shi da mai gadonsa amma kai ake so a miƙa wa wannan dukiya ta hanyar amfani da bayanan da wannan mutumin ya bari na wasiyya cewa, akai dukiyarsa ƙasashen Afrika. Sukan yi amfani da muryar mace ko wani namiji da sunan ma'aikacin baki ko kuma manajan wannan mutumin da ya mutu. Daga ƙarshe za su buƙaci mutum ya tura wasu kuɗaɗe waɗanda za a gyara hanyoyin da kuɗaɗen za su isu wajensa. Wannan wata sabuwar hanyar damfara ce.

#### 4.2.3 Damfara Ta Hanyar Aljannu Masu Taimako

Wannan wata hanya ce da `yan damfara ke amfani da ita da sunan taimako don cutar da jama'a. Yadda suke yin abin shi ne wani ne zai kiraka a waya ya ce, yana buƙatar ka yi wa Annabi Muhammadu (S.A.W) salati, ka karanta wasu ayoyi sai ya umurce ka da ka matsa gefe guda. Idan mutum ya faɗa wannan tarko sai ya ce, "Shi Aljani ne". Daga nan sai ya yabeka ya nuna ka taɓa taimakonsa ko mahifinsa ko wani abu mai Kaman haka shi ne yake so ya saka maka da dukiya mai yawa. Saboda haka zai fara faɗa maka ka yi kaza, ka yi kaza. A ƙarshe ya ce wasu irin kuɗi kake buƙata a taimaka maka da su, misali idan mutum ya ce dalar Amurka yake so, sai ya ce, ka je ka same su ka zuba cikin abu irin kaza a kai wuri kaza, a daidai loaci kaza za su mayar maka da su miliyoyi. Wani lokaci za ka ji sun ce su Aljanu ne daga Makka ka fara sayen kati ka tura masu.

To ko dai mene ne Aljanu ba su magana da mutane ta waya, kuma ba sa buƙatar layin sadarwa domin su yi magana. Hasali ma ba a ganin Aljani kuma ba yin magana da su sai ta bori ko ta Rukiyya, in ba haka ba duk wanda ya ce shi Aljani ne yana magana da mutane kai tsaye to ɗan damfara ne, a kiyaye.

#### 4.2.4 Damfara ta Kutsen Shafin Sadarwa Na Zumunta

`Yan damfarar zamani sukan yi ƙoƙari su saci shafin sada zumunta na mutum su yi amfani da shi wajen yaudarar mutane musamman abokansa da kuma makusantansa. A kan yi magana da abokan mutum a matsayin shi yake yi, sai su yi amfani da wanann damar su nemi taimako na kuɗi na wucin gadi da cewa idan sun haɗu za ya biya. Wani lokaci sukan buƙaci a aika masu da katin waya. Sukan nuna cewa suna wani wuri kuma sun samu matsala don haka suna buƙatar kati. To wanan ma wata hanya ce ta damfara.

#### 4.2.5 Saƙon Albishir Daga Kamfanin Waya

Wata hanya ta damfara a wannan zamani ita ce ta aiko da saƙon albashir daga gidan waya na cewa mutum ya yi nasarar cin wata kyauta ko kuma lambar aka zaɓa a wajen gudanar da wannan gasa kuma ya ci naira miliyan ɗaya da sauransu. Don haka ana buƙatar ka ba da kuɗi kaza kafin a aiko maka da waɗannan kuɗaɗe. To wannan ma wata hanyar damfara ce.

#### 4.2.6 Damfarar Kawo Kuɗi Na Ninka Maka

Wannan hanyar damfara ta shahara a Intanet da zahiri. Wanann wankiya ce tsagwaronta da ake amfani da dabarar buɗe wani kamfani. Za a faɗa cewa wanann kamfani yana harkar sayar da ɗanyan mai da gwal. Don haka idan ka saka hannun jari na naira dubu ɗaya wani mako mai zuwa za su ninika maka ya koma dubu biyu ko fiye da haka.

Haka kuam a Intanet a an ɓullo da wani tsari na kasuwanci wanda ake kira Foreɗ Trading wanda a zahiri akwai su. Amma `yan damfara suna amfani da wanann wajen cutar mutane ta hanyar ƙwaɗaitar da su cewa duk abin da mutum ya sa za a nininka ma shi. Kuma kuɗinka zai riƙa ƙaruwa dangane da yawan mutanen da ka kawo. Sukan yaudari mutane da fara ba mutanen farko domin su yi shigo-shigo ba zurfi. To duk waɗanda suka biyo bayan wannan mutum duk yaudararsu za su yi.

#### 4.2.7 Damfarar Ta Satan Bayanan Sirri

Wannan hanya ce da ae damfara ta amfani da na'urar kwanfuta. Wanann satar bayanai sirri shi ne ake cewa, "Techincal Hacking". Domin kowace kwanfuta tana da abin ɗaukar hoto wanda ƙwararru suke amfani da ita wajen gano bayanan sirri na mutum. Domin babu wani abu da mutum zai yi face suna ganinsa. Sukan yi amfani da wannan damar wajen samun bayanai na siiri da kuma amfani da su wajen damfara. Misali: Mutum yana zaune wata ƙasa yana shiga yanar gizo domin neman bayanan sirri ta hanyar Imail da sauransu. A irin wannan damfarar a kan samu bayanan sirri na banki a shiga cikin asusun masu ajiya a ɗebi kuɗi ba da saninsu [5].

#### 4.2.8 Damfara Ta Amfani Da Na'urar Kamfuta

Masana ilimin kwanfuta na amfani da ita wajen gudanar da damfara. Ana amfani da wannan na'ura a matsayin `yan koren zamani. Bokaye na sanya na'urar kamfuta a wani ɗaki da suke fara ajiye mutane kafin su gane da su. A lokacin da mutum yake wannan wuri duk abin da yake aikatawa suna ganinsa. Don haka da ya zo sai su fara ba shi labarin abin da ya aika a bayan idonsu. Wanann kan ba mutum mamaki ya ɗauka cewa wata baiwa ce ta daban. Don haka du abin da aka faɗa masa sai ya amince nan take.

Haka kuma sukan yi amfani da wannan na'ura wajen faɗa wa mutum wasu matsaloli da yake fuskanta.

[4] Hira da Malam Sani wani wanda ya faxa tarkon `yan damfara.

[5] Hira da wani masanin Kwanfuta a garin Sakkwato a ranar 18/10/2025 na qarfe 10 na safe

© 2026 | Published by Scholars Middle East Publishers, Dubai, United Arab Emirates 

Wannan yana faruwa ne ta hanyar `yank ore. `Yan kore kan zauna su riƙa amfani da tsarin sadarwa na Whatsapp suna ba da bayanin abin da mutum yake aikatawa alhali bai sani ba. Don haka sai `yan damfara su kira mutum su riƙa faɗa masa abin da yake aikawa a halin yanzu. Daga sai su umurce da ya kai wasu kuɗaɗe a wani wuri ko kuma ya aikata wani abu buƙatarsa za ta biya.

#### 4.2.9 Damfarar Neman Aiki

Wannan wani nau'in damfara ce da ake aiwatar musamman ga masu neman aikin gwamnati. A irin wannan damfara akan yi wa mai neman aiki alƙawarin sama masa gurbin aiki a wata ma'aikata ko kuma wata hukuma amma sai a umurce shi da sai ya biya wasu kuɗaɗe na toshiya baki kafin a ba shi takardar ɗaukan aiki. Mafi yawa `yan boko ne masu son samun aiki a ma'aikata mai tsoka wato NNPC ko kuma wani kamfani don haka a kan umuurce su da biyan kuɗaɗe masu tsoka kuma daga ƙarshe ba su ga tsuntsu ba su ga tarko [6].

#### 4.2.10 Damfara Ta Hanyar Wayar Hannu

Ana mafani da wayar hannu wajen gudanar da damfara. Masu yin wannan damfarar sukan kira mutum ne su ce daga bakinsa sannan su bayyana masa sunansa da shekarun haihuwarsa da ranar da ya buɗa asusun ajiya. Daga nan sai su buƙaci ya ba su lambar katin ATM. Wasu kuma sukan nemi lambar sirri na ajiyar kuɗi. Haka kuma wata hanya ita ce wadda ake cewa an kawo wani tsari na taimakonn jama'a. wanda mutum zai ba da kuɗi a ninika masa.misali: MNN Ponzy Scheme wanda aka yi amfani da shi aka damfari mutane da yawa. A halin yanzu an ɓullo da wata hanyar yaudara ta waya wanda za a aiko wa mutum a umurce shi da ya shiya wani tsari wanda daga bisa za a buƙaci ya cike ta hanyar bayar da sunansa da lambar asusun ajiyarsa na banki da sauransu. Da zarar mutum ya bi umurnisu to, shi ke nan za a kwashe duk ajiyarsa a banki.

Akwai kuma hanyar aiko da saƙo da hanyar Imel wanda ake yi wa mutum albishir cewa yana daga cikin wanda gwamnati ta zaɓa da za a ba muƙamai don haka ya turo bayanansa wato CƁ da zarar ya yi sai kuma su aiko masa cewa akwai buƙatar ya aiko da wasu kuɗaɗe domin za a kama masu wurin da za a ba su horo na sanin makaman aiki. Daga ƙarshe sai akai mutane a ajiye a wani hotal wanda bai kai yawan kuɗin da suka aika ba. Kuma irin wannan damfara an fi yi masu ilimi kuma da gogaggun yan boko.

### 4.3 Illolin Damfara

Babu tantama, damfara ba ce mai tattare da illoli masu yawa ga al'umma. Bisa ga bayanai da aka samu ƙalatowa yayin gudanar da wannan bincike sun haɗa da:

a. Haifar da tsiya da talauci: Mutane da yawa sun tsiyace saboda an raba su da abin da suka malla don haka suka faɗa cikin talauci. Kamar yadda Ibrahim, (1982) ya bayana cewa damfara ta haifar da talauci da jefa mutane cikin rayuwar ƙa-ƙanikayi. Wasu ma takan yi sanadiyyar rasa hankulan su ko ma rayuwa baki ɗaya.

b. Sauya Bagirn Arziki: Idan aka damfari mutum duk abin da ya mallaka yakan sauya hannu daga wannan zuwa wancan. Don haka ɗan damfara da arziki sun riski juna ne don ba shi ya nemo shi shi ya sa ake samun lalacewa arzikin da ka samu ta hanyar damfara.

c. Karya tattalin Arzikin Ƙasa: A duk lokacin da aka samu arzikin ƙasa na bin hanyar da bai dace ba, ma'ana haramtacciyar hanya wadda gwamnati ba ta amince da ita ba, to yakan haifar da matsalar tattalin arziki a wannan ƙasa. Domin gwamnati za ta rasa hanyar samun kuɗaɗen shiga. Haka kuma idan ɓarnar damfara ta yawaita tana iya durƙusar da ƙasa nan take musamman `yan damfara na zamani ta hanyar Intanet da ke kai kuɗi ƙasashen ƙetare suna ɓoyewa.

## 5.1 SAKAMAKON BINCIKE

A ƙarshe an fahimci cewa damfara, ruwan dare babu jinsin da ba su yi. Kuma babu wanda ya ƙetare karkonsu sai wanda ya cire wa kansa kwaɗayi da son abin duniya. Binciken ya fito da dabarun bincike na gargajiya da na zamani waɗanda ake amfani da su wajen karɓar kuɗi a hannun mutane. A zamanin da, `yan damfara suna amfani da hanyoyin siddabaru na gargajiya wajen aiwatar da damfara, sannan damfar da su ta danganta ne ga wanda bai san irin siddabarun da suke amfani da shi kuma taƙaita ne a wurin da suke gudanar da ita kawai. Wanda yanzu a wannan zamani damfarar ta ɗauki sabon salo, domin ana amfani da abubuwan da zamani ya shigo da su wajen yaudarar mutane. Nau'o'in damfarar zamani sun haɗa dukan rukunin jama'a da ke cikin al'umma. A damfarar zamani wasu takan rutsa da wasu mutane saboda rashin sani, wasu kuma tsananin kwaɗayi ne ke haifar da shi. Masu damfara sukan yi amfani da sabon tsarin da bankuna suka fito da su, wajen damfarar mutane. Wasu mutane ne kuma suna amfani da wayar hannu domin damfara, yayin da wasu kuma sukan shiga shafukan sadarwa na zumunta na zamani domin damfarar mutane. Sannan damfara mafi muni shi ne wanda ake yi ta hanyar Intanet domin a wannan hanyar miliyoyin daloli ake kwashe a asusun ajiya a sauya masu wuri cikin ɗan ƙananen lokaci. Akasari masu gudanar da wannan damfara ana kirasau da suna, "Yah [7], oo boys". Haka kuma binciken ya fahimci abubuwan da ke haifar da damfara da dalilan yin damfara da illolin damfara. Daga ƙarshe bincike ya gano cewa ba wani abu ke sa a damfari mutum ba sai kwaɗayi wanda Hausawa ke yi wa kirari da mabuɗin wahala. Domin kwaɗayi ya haifar da mutane sun yi hasarar dukiyoyi masu tarin yawa. Don haka ya kamata mutane su kiyaye a duk lokacin da suka

[6] Hira da Malam Munir Sidi a UDUS ranar 20/10//2025.

[7] Wasu qwararrun kuma masana ilimin kwanfuta da sadarwa ta zamani

ga wani wanda ba su fahimci shi ba, ka da su yi saurin faɗawa cikin wannan lamari sai sun tuntuɓi masana.

## 5.2 KAMMALAWA

Damfara ruwan dare ne game duniya. Domin babu lokaci ko yanayin da ba a gudanar da ita. Haka kuma a wancan zamani ana amfani da siddabaru wajen aiwatar da damfara. Sannan kuma `yan kore sun taka muhimmiyar rawa wajen gudanar da damfara. Domin damfara ba ta yi yuwa dole sai an samu ƙwararren ɗan kore wanda zai taimaka wajen turo mutane a damfara su. waɗannan `yan damfara sun haɗa da bokaye da malaman tsibbu da gardawa da sauransu Amma yanzu da aka samu wayewar kai sai damfara ta ɗauki sabon salo. Wato da shiga sahun amfani da abubuwan da zamani ya kawo. Waɗannan na'urorin zamani su ne suke matsayin `yan a sigar damfarar zamia, saboda ta amfani da su ne ake samun bayanai da za a yi amfani da su wajen damfara. Wannan ya ba `yan damfara damar shiga cikin rigar zamani su ci karen su babu babbaka. Waɗannan nau'o'rorin zamani sun taimaka wajen aiwatar da damfara ta yadda wanda aka damfara babu yadda zai gane sai bayan aikin gama ya gama. Damfarar zamani ta ɗauki fuskoki da dama kama daga damfarar satar sirrin banki da ta satar kuɗi a asusun banki da ta amfani da wayar hannu da sauransu.

## MANAZARTA


- Adamu, M. (2012). Cacar Gargajiya A Ƙasar Katsina. Kundin digiri na biyu jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato.
- Adamu, M.T (2014). *Siddabaru A Ƙasar Hausa*. Kano: Century Research and Publication Limited.
- Alhasan, H da Musa, U.I da Zarruƙ, R.M (1982). *Zaman Hausawa*. Bugu na biyu. Zaria: Institute of Education.
- Atuwo, A.A. (2009). Ta'addanci A Idon Bahaushe: Yaɗuwarsa Da Tasirinsa A Wasu Ƙagaggun Rubutattun Labaran Hausa. Kundin digiri na uku jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato.
- Bunza, A.M (1989). Hayaƙi Fid da na ƙogo: Nazarin Siddabaru da Sihirin Hausawas. Kano: Kundin digiri na biyu jami'ar Bayero Kano.
- Bunza, A.M (1994). "Damfara Da 419 A Bahaushiyar Al'ada". (Nazarin Nason Da Damfara A Rubutattun Ƙagaggun Labaran Hausa). Takarda da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sakkwato.
- Bunza, A.M (1998). Siddabarun Ƙoƙuwa Da Birkita Kwanci. Maƙala da aka gabatar a sashen koyar da harsunan Nijeriya jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sakkwato.
- Doma, A.A (2018). Damfara A Al'ummar Ƙasar Kwantagora. Kundin digiri na farko. Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.
- Ibrahim, M.S (1982). Dangantakar Al'ada Da Addini. Kundin digiri na biyu jami'ar Bayero Kano.
- Kundin Digiri na biyu jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sakkwato.
- Maiyama, U.H (2001). Jogon Sata A Cikin Wasu Rubutattun Ƙagaggun Labaran Hausa. Kundin digiri na biyu jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato.
- Sa'id, B. (*Edita*) (2006). *Kamusun Hausa*. Kano: Jami'ar Bayero.
- Sani, A-U & Yusuf, J. (2024). Gani Ga Wane...: Kasuwancin Damfara a Kan Intanet. East African Scholars J Edu Humanit Lit; Vol-7: Iss-12 (Dec, 2024): 392-399
- Sani, H (2019). Hanyoyin Damfara Masu Wahalar Ganewa. http//.duniyar computer/mai-amf. Retrieved 0n 22/10/2025.
- Usman, B.B (2000). Damfara Da Yaudara A Maganin Gargajiya a cikin *Degel Journal of Arts and Islamic Studies*. Vol. 111. Sakkwato: Usmanu Ɗanfodiyo University.
- Wushishi, S.S (2011). Dangantakar Magani Da Wasu Sana'o'in Gargajiya Na Hausawa.
- Yahya, A.B (1994). Matsayin Waƙoƙin Baka A Cikin Adabin Baka. Muƙala da aka gabatar a Makarantar Mata W.A.T.C Gusau.
- Yahya, A.B (1996). In Praise of Thieves: And Old Category in Oral Portry. Muƙala da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani, Tsangayar fasaha da Addinin Musulunci, jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato.